# DEUTSCHE WELLE
# JI KA KARU

## Kowa dabam Allah ya yi shi: Mutunta haƙƙin tsirarru
## Kashi na takwas: ’Yan ƙabilar San a Botswana da fafutukarsu ta neman muhalli


| | |
|---|---|
| Wanda ya rubuta: | Adrian Kriesch |
| Wanda ya fassara: | Ɗanlami Bala Gwammaja |
| Wadda ta tace: | Halima C. Schmaling |


**’Yan Wasa:**

Mai ba da labari

| | |
|---|---|
| Roy Sesana: | ɗan shekara 60 |
| Jumanda Gakelebone: | ɗan shekara 35 |
| Sithilo Thekiso: | ɗan shekara 45 |
| Mosalagadi Mowawaphuti: | ’yar shekara 45 |
| Mabele Owa: | ɗan shekara 60 |

**Mai gabatarwa:**

Masu saurarenmu, barkanmu da sake kasancewa da ku a cikin kashi na takwas na shirinmu na "Ji Ka Karu" mai suna "Kowa Dabam Allah Ya Yi Shi - Mutunta Haƙƙin Tsirarru". A cikin jerin shirye-shiyen namu muna ta haɗuwa ne da mutane waɗanda yanayin rayuwarsu, da siffofinsu, da kuma yadda suke tunani suka sha bamban da na sauran mafiya rinjayen al'umma. A saboda wannan yanayi nasu na rayuwa sukan fuskanci wariya da ƙyama, amma kuma duk da haka sun ci gaba da fafutukar ganin sun ƙwaci haƙƙinsu.

A shirin namu na yau, za mu nufi ƙasar Botswana ne inda za mu gana da mutanen wata ƙabila 'yan asalin ƙasar ta Botswana. Wannan ƙabila dai ana kiranta da suna San, a wasu lokutan kuma ana kiran 'yan kabilar da suna 'Bushmen', wato ƙauyawa. Su 'yan wannan ƙabila tun shekaru aru-aru suke da zama a tsakiyar dajin Kalahari. Wani ƙauli ma cewa yake, 'yan wannan ƙabila su ne mutanen farko a nahiyar Afirka. Sai dai kuma a kusa-kusan nan, gwamnatin ƙasar tasu ta yi yunƙurin tilasta musu barin yankunan da suke zaune, amma sai suka turje. A maimakon haka ma sai suka shiga fafutuka ta lumana don ƙwato haƙƙinsu na wuraren samun ruwa da kuma gonakinsu, kuma sun samu nasara a wannan fafutuka da suke yi.

**Bayanin Roy Sesana cikin San:**

*"Sunana Roy Sesana, ni ɗan shekara 60 ne da haihuwa. An haife ni ne a wannan daji na Kalahari, kakana ma da babana da yayyena duk a nan aka haife su. Wurin da muke da zama wuri ne mai kyau, ƙasar wurin jigawa ce, kuma ga sarari ko'ina. Yankin namu ya ma fi kyau a lokacin damina, lokacin akwai furanni masu ban sha'awa. Ku mutanen cikin birni kuna da kantunan yin sayayya inda kuke sayen komai da komai. Ni ma a nan cikin daji babu abin da ba zan iya samu ba. Zan iya zuwa na haƙo abinci kamar rogo ko dankali idan ina jin yunwa, ko kuma na samo kankana. Haka kuma zan iya fita farauta. Zan so a ce tattaɓa kunnena ma a nan za su rayu kuma su mutu a nan."*

**Mai ba da labari:**

Roy ya tashi cikin alfahari yana nuna mini yadda wannan wuri da yake da zama yake. Ana kiran wannan ɗan karamin ƙauye Molapo. Wannan ƙauye dai cike yake da bukkoki, kuma yana nan ne a tsakiyar gandun dajin Kalhari. Yanzu iskar bazara sai kaɗawa take yi, duk ta bule mana idanuwanmu da yashi. Roy ya gayyace mu cikin bukkarsa wadda aka yi ta da katakwaye, da rassan itatuwa, kuma aka rufe da jinka. Roy cike yake da farin cikin sake dawowa wannan ƙauye. Wannan fa wani abu ne da sai da ya daɗe yana fafutuka a kansa.

A cikin shekarar 1997 an tilasta wa mazauna wannan gandun daji da su sauya matsuguni. Gwamnatin ƙasar Botswana ta yi da'awar cewa ba za a iya kare wannan gandun daji ba, matsawar mutane suna zaune a cikinsa. Roy shi da sauran masu fafutukar siyasa sun sha ɗaukaka ƙara a kotu a kan wannan matsayi na gwamnati. Sai a shekara ta 2006 ne suka samu nasara a kan wannan ƙara tasu. An ba 'yan asalin mazauna wurin damar dawowa matsuguninsu. Wannan dai ba ƙaramar nasara ba ce ga 'yan ƙabilar San, kuma wannan shari'a ta ja hankalin duniya. Sai dai kuma kamar yadda Roy ya bayyana mana, da sauran rina a kaba.

**Bayanin Roy Sesana cikin San:**

*"Duk da cewa kotu ta fito fili ta bayyana cewa doka ta ba mu damar zama a yankunan nan namu, amma har yanzu gwamnati na kawo mana matsala. Mu dai mafarauta ne, amma kuma yanzu babu dabbar da za mu farauto. Gwamnatin ta yi mana alƙawari lasisi na musamman da zai ba mu izinin yin farauta, har yanzu ba mu samu ba. Kuma ga shi ba sa ba mu abubuwan more rayuwa kamar su ruwa da sauransu. A ƙarshe dai sai da muka sake gurfanar da gwamnatin a gaban kotu."*

**Mai ba da labari:**

Yankin da Roy yake zaune dai tare da iyalinsa yana da girma. Wannan gandun daji dai da ake magana a kansa ya kai girman ƙasar Ruwanda da Burundi gaba ɗaya. Sai dai kuma babu isasshen ruwa a wurin, musamman ma dai a lokacin rani. An ba wa 'yan asalin mazauna wannan yanki damar dawowa

matsugunansu, amma kuma gwamnati ta haramta musu gina rijiyoyi. Don haka sai 'yan ƙabilar San suka sake garzayawa kotu. Sun sake samun nasara a wannan ƙara da suka kai a cikin shekara ta 2011. Gwamnati ta rungumi wannan hukunci da kotun ta yanke, amma fa kuma ta ce ba za ta taimaka ba wajen gina rijiyoyin. Wannan aiki na gina rijiyoyin ƙungiyoyin da ba na gwamnati ba ne suka taimakawa wajen yinsa, da kuma wani kamfanin haƙar ma'adinai mai suna 'Gem Diamonds'. An dai haƙa rijiyoyi a yankuna dabam-dabam har ma da ƙauyen na Molapo.

Jumanda Gakelebone wani matashi ne ɗan shekara 35 da ya shafe shekaru masu yawa yana fafutuka kafaɗa-da-kafaɗa da su Roy wajen ƙwato haƙƙin 'yan ƙabilar San. A cikin bayanin da ya yi mana, ya nuna mana wani butut da aka shimfiɗa a ƙarƙashin ƙasa, yana cewa:

**Bayanin Jumanda Gakelebone cikin Turanci:**

*"Wannan ita ce rijiyar burtsatsen da kamfanin 'Gem Diamonds' ya haƙa a shekarar da ta wuce. Abin takaicin shi ne, rijiyar ba ta ba da ruwan kirki. Idan da za ta dinga bayar da ruwa sosai, da rayuwar mutanen wannan yankin ta inganta. Kuma mutanen da suka ƙaurace wa wannan wuri duk za su dawo. Kuma mutane za su daina samun matsala a lokacin rani."*

**Mai ba da labari:**

Duka-duka dai rijiyoyin burtsatse guda huɗu aka haƙa a wannan gandun daji, amma kuma a halin yanzu ɗaya ce kawai take bayar da ruwan da mutane za su iya sha. Nisan inda rijiyar take ya kai kilomita 100 daga ƙauyen Molapo wanda ya yi wa mazauna gandun dajin nisa. Don haka dole sai sun ci gaba da tara ruwa idan damina ta zo wanda za su dinga amfani da shi har na tsawon shekara guda.

Sithilo Thekiso wani mutum ne ɗan shekara 45 wanda a yanzu haka ga shi nan yana zaune kusa da wannan rijiyar burtsatse da ke Molapo yana ɗan shaƙatawa. Yana yi wa gonarsa shinge ne domin kada dabbobi su dinga shiga suna ci masa amfani. Kamar dai kowane ɗan ƙauyen Molapo, shi ma Sithilo ga shi nan sanye da 'T-shirt' da kuma dogon wando. Waɗannan dai ba su ne kayan sawarsu na gargajiya ba. A da dai Sithilo ya kasance maharbi ne, amma

yanzu gwamnati ta haramta yin farauta. Yanzu dai ya samu ya dawo wannan yanki bayan da gwamnati ta tilasta musu barin wurin.

**Bayanin Sithilo Thekiso cikin San:**
*"Gaskiya na fuskanci matsalar rayuwa. Ban saba da can yankin da na koma ba. Idan da a nan ne, da aƙalla zan iya zuwa na haƙo rogo ko dankali, na kuma yi noma don samun abinci. Amma a wancan yankin da muka koma haka ba za ta yiwu ba."*

**Mai ba da labari:**
Sithilo da matarsa Mosalagadi Mowawaphuti sun fi sabawa da rayuwar ƙauye, kuma sun fi ganin cewa rayuwarsu za ta fi kyau ne idan suna ƙauyen na Malapo. Sun yi farin ciki sosai da kotu ta ba su damar dawowa yankunansu na haihuwa. Kamar yadda matar tasa, Mosalagadi, ta bayyana, ko ba komai sun samu damar baro can yankin da aka mayar da su mai suna New Xade.

**Bayanin Mosalagadi Mowawaphuti cikin San:**
*"Ni ban saba da rayuwar wannan yanki na New Xade ba, ba ta da daɗi. Shi ya sa ma na dawo nan. 'Yata ɗaya ce kawai yanzu haka tana can da zama, kuma gaskiya ina begenta. Ni ban san yadda zan shawo kanta ta dawo ba."*

**Mai ba da labari:**
Daga cikin mutanen da aka tilasta wa barin wannan yanki, bai fi rabinsu ba ne suka dawo wannan gandun daji a yanzu. Yawancin waɗanda suka dawo ɗin tsofaffi ne dai da ƙananan yara. Yanzu haka dai akwai 'yar Sithilo mai shekara 18 da ta yi zamanta a sabon matsugunin nan na New Xade. Domin jin dalilin da ya sa ta ƙi dawowa, mun yi tattaki zuwa can New Xade ɗin, wanda ɗaya ne daga cikin yankuna uku da aka tanada domin sake tsugunar da 'yan wannan ƙabila.
Wannan tafiyar dai ta ɗauke mu awa shida kafin mu kai ga wannan ƙauye wanda ba a cikin gandun dajin yake ba. A wannan ƙauye dai gwamnati ta tanadar da muhimman abubuwan more rayuwa: akwai asibiti, da makarantu, da kuma gidajen jami'anta. Su kuwa 'yan ƙabilar San da aka dawo da su nan

suna zaune ne a bukkokinsu na gargajiya.

Ita dai ƙasar, Allah Ya albarkace ta da arziƙin ma’adinai. Kuma ba kamar sauran ƙasashen Afirka ba inda manyan ƙasa kan arzurta kansu kawai, shugabannin wannan ƙasa baya ga arzurta kan nasu haka kuma sun zuba jari wajen ci-gaban wannan ƙasa.

Manufar yin haka shi ne, domin a sama wa ’yan ƙabilar ta San ilimi da kiwon lafiya. Wannan fa zai yiwu ne kawai idan suna zaune a sabon matsugunin da aka tanadar musu, ba wai a ce suna warwatse a ƙauyukan da ke cikin gandun dajin ba. Ɗan fafutukar ƙwato ’yancin nan, wato Roy Sesana, da ke ƙauyen Molapo, tuni ya riga ya san haka. Shi a wajensa muhimmancin da ilimi yake da shi daidai yake da na zama a mahaifar mutum.

**Bayanin Roy Sesan cikin San:**

*“Dole ne mutanen da aka matsa wa su tashi su nemi haƙƙinsu. Kasar haihuwa tana da muhimmanci sosai kamar dai iyaye take. A nan ne aka haife ka, a nan ne ka tashi, kuma a nan ka zama duk abin da ka zama.”*

**Mai gabatarwa:**

Da waɗannan kalamai na Roy Sesana, ɗan fafutukar kare haƙƙin ’yan ƙabilar San muka kawo ƙarshen shirin namu na “Ji Ka Karu” a yau, wanda muka kawo muku daga ƙasar Botswana. Wakilinmu Adrian Kriesch ne ya kawo mana wannan rahoto. Idan kuna son jin sauran rahotannin da ke cikin jerin wannan shiri a kan mutunta haƙƙin tsirarrun mutane, sai ku ziyarci adireshinmu na yanar gizo, wato dw.de/lbe. Kazalika muna maraba da muhawara da ku a shafinmu na ‘Facebook’. Kar kuma ku manta, ku kasance da mu a shirinmu na gaba. Ku huta lafiya!